Bijochs: Dec, 2025 Vol. 3 - Issue, 2 ID No. 010 (Pg. 107-115)

# Tarken Jigon Addini Cikin Wasu Waƙoƙin Malam Nasir Garba Ahmad 'Yan'awaki

**Dr Musa Isah Abubakar**
musaisahabubakar@yahoo.com
07064833646, 07066585353
Tsangayar Harsuna
Sashen Koyar da Hausa
Kwalejin Ilimi ta Jihar Jigawa, Gumel.

***Tsakure***

*Jigon Addini a cikin rubutattun waƙoƙi wani fage ne kandamau da marubu na baya da na yanzu suka yi rubuce-rubuce a kansa. Hakan ya wanzu tun daga ƙarni na 17 zuwa ƙarni na 18, da 19, da 20 har zuwa wannan ƙarni na 21 da muke ciki. Saboda haka wannan takarda za ta yi tsokaci ne dangane da Tarken Jigon Addini Cikn Wasu Waƙoƙin Malam Nasir Garba 'Yan'awaki. Cikin wannan takarda za a yi ƙoƙarin kawo ma'anar. Bayan nan kuma za a kalli taƙaitaccen tarihin wannan mawallafin waƙoƙi tare da ɗaukar wasu daga cikin waƙoƙinsa da suka shafi Addini domin yi masu tarke na ƙwaƙwaf domin fitar da jaki daga duman suruka. Daga ciki waƙoƙin zaɓi waƙar Bayanin Layya don yin tarken jigon addini.*

***Keɓaɓɓun kalmomi:*** *Tarke, Layya Jigo, Addini*

## 1.0 Gabatarwa

Waƙa hanya ce ta isar da saƙo cikin sauƙi. Wannan hanya ta isar da saƙo cikin sauƙi an yi amfani da ita tun a wajen ƙarni na 17 zuwa ƙarni na 18 lokacin da Wali Ɗanmarina da Wali Ɗanmasani suka yi rubuce-rubuce da suka haɗa da waƙoƙi. A ƙarni na 18 an sami ayyukan irin na su Malam Muhammadu Na Birni Gwari da Malam Muhammadu bn Muhammadu Al – Katsinawi da Malam Shitu Ɗan Abdurra'uf. Hakazalika a ƙarni na 19 lokacin Jihadi Shehu Usmanu Ɗanfodiyo tare da almajiransa sun yi amfani da wannan hanya ya isar da saƙo wajen jaddada Addinin Musulunci. Idan mun dubi waɗannan ƙarnuka da suka shuɗe za mu tarar cewa dukkanin waƙoƙin da aka rubuta jigoginsu na Addini ne da suka haɗa da yabo da Fiƙihu da Tauhidi da Siyasar Musulunci da sauransu.

### Ma'anar Tarke

Kalmar tarke bisa asalinta kalma ce ta Larabci wadda su Larabawa suke ce ma Tarƙe. Amma da ta shigo cikin Hausa sai malamanmu musamman na soro suke kiran ta Tarke wadda ma'anar wannan kalma da Hausa ita ce Hauhawa. Waɗannan malami sun kafa hujja ne da lokaci da aka yi tafiya ta Isra'i da Mi'iraji da Annabi S.A.W. zuwa sama inda aka hau da shi hawa-hawa har zuwa sama ta bakwai, shi ne shahararren mai waƙen nan na Ishirinya Malam Alfazazi yake cewa:

'Taraƙƙa bi hi baynas sama'i Manzila'

Ma'ana "An hau da shi wurare tsakanin sammai".

Ta ɓangaren nazarin adabi kuwa, masana da dama sun bayyana ma'anar 'Tarke' gwargwadon fahimtarsu. Daga cikinsu akwai:-

Ɗangambo (2008:2), "keɓaɓɓiyar hanya ce da ke nufin tsara sharhi a kan wani matani ko wani abu da aka nazarta ta bin ƙa'idojin nazari da manazarta suka tsara bias ra'ayi".

Gusau, (2015) ya bayyana tarke da cewa "wuri ne inda ake warware matsaloli na Mazhaba tare da ɗora su kan wani ɓangare matanin adabi ko al'ada. Sannan da yin sharhi da tsokaci da kuma fifita wani ra'i ko Mazhaba bida ƙarfafa hujjoji a kan bin da aka zaɓa. Ya ci gaba da cewa tarke ilimi ne na nazari wanda ya yake a tsakanin matanin adabi da ra'ayin adabi a yayin da ake ɗora shi a kan adabi, ko ya zama tsakanin wani abu na al'ada da kuma ra'i ko ra'ayoyin masana kan al'ada"

Shu'iabu, (2017) ya bayyana tarke da "naƙaltar aikin adabi da bin diddiginsa don a ƙalailaiceawasu tunane-tunane da saƙonnin da ke ckinsa ta hanyar amfani da ilimin mai tarke da yanke hukuncinsa a kan ra'ayoyin masana don fito da tasirin aikin adabi ga jama'a". Shi kuwa Read (1956:124) yana ganin tarke a taƙaice shi ne harkar ƙimanta matsayin adabi ta amfani da wasu ƙa'idoji ko matakai.

Ado, (2017) ya bayyana tarke da cewa shi ne wata dabara ce da masu ilimi ke yi don yin sharshi ko kushe ko kawo ƙarin bayani a kan wani batu na ilimi.

Ta wani ɓangaren za a iya cewa 'Tarke' shi ne ƙirƙiro wata hanya mai muhimmanci ta yin nazarin adabin Hausa musamman kana abin da ya sahafi matani waƙoƙi ko zube ko kuma wasan kwaikwayo. A taƙaice 'Tarke' wataa hanya ce da ake amfani da ita wajen yin sharhi ko wani abu ba sai na littafi ba.

## 1.1 Tarihin Rayuwar Malam Nasiru Garba Ahmaad 'Yan'awaki

An haifi Nasiru G. Ahmad a unguwar 'Yan'awaki da ke cikin birnin Kano a ranar Lahadi, 16 ga Safar, 1384 BH, wanda ya yi daidai da 4-2-1964 Miladiyya. Ainihin sunansa shi ne Nasiru Ahmad Garba. A lokacin karatu Ahmad ɗin ya so ɓacewa saboda taƙaita shi da A. da akan yi, don haka aka mayar da shi ƙarshe. Kakansa Alhaji Garba Maigoro, yana cikin fitattun 'yan kasuwa da aka yi a unguwar Zangon Barebari, wanda a wannan unguwar aka haifi mahaifin Nasiru Garba Ahmad da sauran 'yan'uwan mahaifin nasa masu yawa. Zama ne ya kai mahaifin Malam Nasiru unguwar 'Yan-awaki a inda aka haifi Malam Nasiru Garba Ahmad a can. Mahaifiyarsa haifaffiyar unguwar Lalloki ce da ke cikin birnin Kano. Kamar yadda ya bayyana, kakanninsa duka Barebari ne, bai san tun lokacin da suka zo Kano ba. Shi ne ɗa na goma a wurin mahaifinsa, amma ya taso tare da 'yan'uwa huɗu; maza uku da mace ɗaya. A yanzu duk sun rasu, saura shi kaɗai ya rage. Ya yi ƙuruciyarsa ne a unguwannin Koƙi da 'Yan'awaki. Ya zauna a unguwar Koƙi ne a wurinyayarsa, tun ana ɗaukarsa a kafaɗa a kai shi, da yamma a dawo da shi, har ta kai ga ya iya zuwa da kansa.

A halin yanzu Malam Nasiru Garba Ahmad yana zaune ne a gidansa da ke yankin Maidile, Karamar Hukumar Kumbotson jihar Kano, a inda yake zaune da matarsa guda da 'ya'yansa. Mutum ne mai sha'awar

shiga harkokin jama'a, amma masu ma'ana da manufa mai amfani. Ba kasafai yakan shiga hira barkatai ba, hakan ne ma ya sa a mafi yawan lokuta, idan ya taso daga aiki ba inda yake zama sai a gida, sai fa in ta kama zai fita zuwa wani wuri. Malam Nasiru yakan ziyarci duk wanda suke wata hulɗar alheri da shi, ko da shi ne gaba da shi. Yana iya ƙoƙarinsa wajen amsa wa duk wanda ya gayyace shi wani sha'ani nasa. Yana bakin ƙoƙari wajen cika duk alƙawarin da ya ɗaukar wa wani. Yana kuma saɓawa da duk wanda ba ya cika alƙawariMalam Nasiru Garba Ahmad ya fara karatun makarantar allo ne a lokacin da yake hannun yayarsa a unguwar Koƙi a inda ya fara halartar makarantar Malam Ado da ɗan'uwansa Malam Hudu. Daga baya ya ci gaba da karatun allo a 'Yan'awaki wato a makarantar Malam Umaru Gurgu, har ya iya rubuta allonsa da kansa. Malam Nasiru Garba Ahmad ya shiga makarantar Firame Islamiyya ta 'Yan'awaki a shekarar 1975 zuwa 1981 bayan nan sai ya halarci Makarantar Nazarin Addinin Musulunci mai zurfi ta Shahuci (Aliya) a shekarar 1981 zuwa 1987.

Bayan wannan, sai ya halarci Makarantar Nazarin Shari'ar Musulunci ta Aminu Kano, inda ya samu Diploma a harsunan Larabci da Hausa da Nazarin addinin Musulunci, a cikin shekarar 1986 zuwa 1989. A shekarar 1992 ya yi Jami'ar Musulunci ta Madina/ Kwas (Daura) a jami'ar Bayero. Sannan kuma, Malam Nasiru Garba Ahmad ya halarci Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo ta Sakkwato, a inda ya yi karatun digirin farko a kan harshen Hausa daga shekarar 1993 zuwa 1996. A 1999 ya yi wani kwas na karatun gida ƙarƙashin "Sincere Writers Club," inda ya samu takardar shaidar karatu (Certificate) kan aikin jarida. Ya yi karatu a "Alliance Francaise de Kano" inda ya samu takardar shaidar kammala karatu (Certificate) kan harshen Faransanci a shekarar 2002 (Janairu zuwa Disamba). A 2008 ya yi karatu a "I.H.D.I.T." da ke Tarauni, Kano, inda ya samu takardar shaidar kammala karatu (Certificate) da kuma Diploma a 2011 kan sarrafa na'urar kwamfyuta, sannan kuma ya yi karatu a Administratiɓe Staff College of Nigeria (ASCON) a cikin shekarar 2006. Bayan nan kuma ya yi karatun digirinsa na biyu a kan Hausa daga shekarar 2009 zuwa 2014.

Daga cikin malaman da Malam Nasiru Garba Ahmad ya yi karatun gida a wajen su akwai, Marigayi Malam Lawan Mu'azu Zangon Barebari, da Marigayi Malam Sani mai Bandiri Dukawa, da Malam Habibu Ibrahim Usman Zangon Barebari (Alƙali a yanzu), da Sheikh Umaru Ta'ambu Abdullahi da Malam Sadiƙ Maisikeli. Daga cikin Malamansa na makarantun zamani kuma akwai, Malam Aminu Yola da Alƙali Bashir da Malam Sagir Sulaiman, da Malam Ibrahim Abubukar Ramadan (Malam Karami), da Malam Aliyu Hamza Darma da Malam Yusuf Uba Mandawari. Haka kuma, daga cikin Malamansa na Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo ta Sakkwato akwai Farfesa Isa Mukhtar, da Farfesa Aliyu Muhammad Bunza, da Farfesa Abdullahi Bayero Yahya, da Farfesa Atiku Ahmad Dumfawa, da Farfesa Abdulhamid Ɗantumsh,i da sauransu. A Jami'ar Ahmadu Bello Zaria kuma akwai Farfesa Ɗalhatu Muhammad da Farfesa Sa'idu Muhammad Gusau da Dakta Bello Alhassan da sauransu.

Sana'ar Malam Nasiru Garba Ahmad ita ce koyarwa wadda ya fara cikin shekarar 1984, tun kafin ya gama makarantar gaba da firamare, har zuwa yanzu da yake matsayin mai duba malamai (Inspector) a sashen kula da ilimin Larabci da addinin Musulunci na ma'aikatar Ilimi ta jihar Kano.

Malam Nasiru Garba Ahmad ya fara rubutun waƙa ne a cikin shekarar 1983, wanda a wannan shekarar ne kuma ya rubuta wani littafin addini cikin Ajami don koyar da yara. Sannan kuma ya rubuta wani wasan kwaikwayo wanda suka naɗa a rikoda shi da abokansa, suna kwaikwayar yadda ake wasan kwaikwayo da ake yi a rediyo. Malam Nasiru bai gaji rubutun waƙa ba, haka nan ya tsinci kansa yana yi. Koyarwa ce dalilin fara waƙarsa. A lokacin da yake koyar da yara 'yan makarantar Islamiyya ta dare tun 1982.

Jawabi: A daidaita yin amfani da sakin layi sannan a rege a rairaye wannan tarihi.

**1.2 Tarken Jigogin Cikin Waƙar Bayanin Layya.**

Daga cikin waƙoƙin da aka zaɓa za a yi tarken ita ce : Waƙar Bayanin Layya.

Idan an dubi wannan waƙa baki ɗayanta babban jigonta shi ne Addini. Shi jigon Addini kamar Bakandame ne, ko kuma mu ce dunƙulallen jigo ne wanda za a iya kasa shi zuwa jogogi da dama sannan za a iya samun waƙoƙi masu ɗimbin yawa a kowane aji. misali Wa'azi da Ta'aziyya da Yabo/ Madahu da Siyasar Musulunci da Tashin Alƙiyama da Tunatarwa A Kan Mutuwa da sauran su. To wannan waƙa da za a yi tarkenta za ta iya faɗawa kan ɗaya daga ciki waɗancan jigogi da aka zayyano a sama.

**1.4 Waƙar Bayanin Layya**

Kamar yadda muka sani cewa layya wata sunanna ce mai ƙarfi ackin addinin Musulunci. Kamusun Harshen Hausa (2014:332) ya bayyana wannan kalma ta layya da cewa asalinta Kalmar Larabci ce daga "Al- urhdhiya". Sannan yaƙa cewa suna ne na mace, da take nunfin yakan rago ko yardajjiyar dabba ranar bikin gama sauka Arfa, watau ranar goma ga watan Zul-Hajji a addinin Musulunci.

Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero, Kano (2006:304) ya bayyana ma'anar kalmar layya da yankan dabba da ake yi don ibada ranar goma ga watan Zul-Hajj, watau watan da Musulmi ke tafiya aikin Hajji.

Ko shakka babu, za mu iya kallon jigon wannan waƙa a matsayin jigo jumla, domin kuwa tun daga farkon ambaton sunan waƙar wato "Bayanin Layya" mai karatu ko saurare zai fahimci babban saƙon da ake son isarwa shi ne bayani a kan layya. Amma wannan saƙon ba zai fito fili ba yadda za a iya fahimtarsa sai an bi baitocin waƙar ciki da bai domin samun damar zaƙulo abubuwan da za su iya zama hujja.

Wannan mawallafi ya fito da saƙon da da yake son isarwa a cikin baiti na huɗu domin nuna wa mai sauro ko karatu bayani kan layya shi ne saƙon da yake son isarwa. Hausawa kan ce "waƙa a bakin mai ita fta fi daɗi".

> 4. Yau ɗan batu ne ƙwarya-ƙwarya
> na shirya,

Bisa bayanin Layya don mutunawa.

Sannan a baiti na biyar zuwa baiti na takwas ya yiwa Musulmi bayani kan cewa layya sunna ce mai ƙarfi ga mai wadata a wajen babba ko yaro ko jinsin maza ko mata, amma ba a amince ga wanda ba shi da ƙarfi ya yi ba.

5. Sunna hukunci layya ya ikhwani,
   Ga duk Musulmi ɗa ku janye bawa.
6. lla mutum ne baligi koyaro
   Ku bar batun jinsi ku daina rabewa.

A tsakanin baiti na tara mawallafin ya bayyana wa al'umma irin dabbobi da suka halatta a yi amfani da su wajen yin layya

9. Anai da tumaki awaki shanu.
   Kazaka raƙumi ana yankawa.

Hakazalika mawallafin waƙar ya kawo wasu matakai kwanaki ko watanni da shekaru da ya kamata dabbobin da za a yanka domin yin layya su kasance suna da su kafin a yanka su, wannan kuwa ya zo ne a baiti na goma zuwa baiti na goma sha uku

10. Layyar tumaki sai fa ta yi a ƙalla,
    Wata takwas raye tana zagayawa.
11. Amma awaki shekararra aka so,
    Har ta shiga ta biyu take gamsarwa.
12. Shanu ko sai sun uku shekarunta,
    Har ta shiga ta huɗu ake yankawa.
13. Su kuwa raƙumma ya zam ta yi biyar,
    Har ta shiga ta shida take fa isarwa.

Idan mun dubi waɗannan baitoci na sama za a tarar cewa mawallafin yana so ne ya bayyana sharuɗɗa da ya kamata tumaki su cika kafin a yanka su domin yin layya. Daga cikin sharuɗɗan nan dole ne tunkiya ko rago ya kai watanni takwas da haihuwa sanna kum ya kasance suna da ƙoshin lafiya ba tare da wata larura ba. Wannan kuwa ya bayyana ne a baiti na 10.

A baiti na 11 kuma yayin ƙoƙarin bayyana irin sharuɗɗa da ya kamata awaki su cika kafin a yi layya da su. Ga ma abin da yake cewa:

11. Amma awaki shekararra aka so,
    Har ta shiga ta biyu take gamsarwa.

Amma baiti na12 sai ya yi ƙoƙarin bayyana mana manufarsa ta hanyar kawo adadin shekarun da da aƙalla shari'a ta gindaya domin yin domin yin layya da shanu. A nan ya nuna wajibcin sai shanu sun kai shekaru biyu zuwa huɗu kafin a yi layya da su.

12. Shanu ko sai sun uku shekarunta,
    Har ta shiga ta huɗu ake yankawa.

A cikin baiti na sha uku kuma sai mawaƙi ya ci gaba da shelanta wa masu sauraro dangane da adadin shekarun da raƙuma za su kai kafin a yi layya da su. Bayan yagama lissafo ire-iren dabbobin da kuma shekarun da ya kamata a yi layya da su, sai kuma ya gangaro kan irin darajojin da abubuwa da za yanka domin layya suke da su. Bayanan waɗannan darajojin kuwa sun zo ne a tsakanin baiti na 14 zuwa baiti na ashirin. Ga ma abin da yake cewa a waɗannan baitoci:

14.Wajen darajar layya farko rago,
Sannan fiɗiyayye abin dandaƙewa.
15. Sai ta matarsa tunkiya ai kenan.
Sannan a sanyo bunsuru mai ɓewa.
16.Sai dandaƙaƙƙen bunsuru mara ɓewa,
Sannan akuya kar mu zam mancewa,
17. Daga akuya kuma sai bajimin sa,
Ko raƙumi namiji wajen darajawa.
18. Sai dandaƙaƙƙen sa zama zololo,
Sai Saniya haka taguwa ka biyewa.
19. Kima ta dabba a wajen yin layya,
Daɗi na nama shi ka fifitawa.
20. Wato akasin hadaya daimke nan,
A can yawan nama ake dubawa.

Idan mun dubi waɗannan baituka da idon basira za mu tarar da cewa mawaƙin ya fara ne da nau'in bambancin jinsunan na dabobin da kuma yananyin ajin da matsayinsu. Kamar yadda ambata a cikin waƙar Rago shi ne a matakin farko na ƙololuwar daraja a wajen layya, sannan kuma ya kasance lafiyayyar mazakuta ba dandaƙaƙƙe ko fiɗiyayye ba, kuma namiji. Daga nan kuma sai tunkiya ta mata ita ta biyo bayansa ta fuskar daraja, bayan tunkiya kuma a wajen daraja sai Ɗan Taure (bunsuru) sai kuma akuya daga akuya sai Sa bajimi da kuma Saniya ta mata a ƙarshe sai sai Taguwa (Raƙuma).

Wani abin lura cikin wannan bayani da mawaƙin yake na darajar kan dabbobin da za a yanka domin yin layya shi ne inda ya nuna cewa ƙimar dabbar ta shafi daɗinta. Wannan kuwa ya zo ne a baiti na19 zuwa na ashirin. Gga ma abin da yake cewa:

19. Kima ta dabba a wajen yin layya,
Daɗi na nama shi ka fifitawa.

A Wannan baiti mawaƙin yana fifita daɗin nama ta fuskar sadaukar da niyya a wajen Ubangiji, wadda wannan daɗin kan yi zama silar ƙima a wajen Ubangiji da kuma mai yin layyar. To amma da ya zo baiti na 20 sai nuna mana cewa a wajen hadaya ba a duba daɗin naman a'a ana duba yawansa ne.

20. Wato akasin hadaya daimke nan,
A can yawan nama ake dubawa.

A ƙoƙarin fito da wannan manufa tasa mawaƙin ya karkata akalar tunaninsa wajen ganin ya yi wa mai karatun ko sauraro bayani dangane da irin dabbobin da shari'a ba ta amince a yanka ba lokacin layya. Wannan bayani nasa ya zo ne a baiti na 21 zuwa baiti na 27.

21.Dabbar da ta zam mai ido ɗaya jal,
Da 'yar makau layyarsu ba ai yowa.
22. Maririya dabba fa kadda a yanka
Da ke ta cuta tun gaban warkewa.
23. 'Yar gurguwa ma ba yin layyarta,
Kaza ƙumƙmaila mara man lasawa.
24. Akwai hilafar malamai bisa,
Dabbar da jelarta ta zam gutsurewa.
25. Kaza idan kunne nata ya tsage,
Ko kuwa dungulimi abin yankewa.

26. Layya da dabba mai ƙaho ɗaya a'a,
    Ko ko ƙahon nata ya zam karyewa.
27. Waɗannan aibobi idan an samu,
    Gun malamai shi ne abin saɓawa.

Daga cikin dabbobin da shari'a ba ta amince a yanka su domin yin layya ba da wannan mawaƙi ya bayyyana domin cikin waɗannan baituka domin fito da jigon waƙarsa sun haɗa da dabba mai ido ɗaya jal, da kuma dabbar da ta gamu da cuta bayyananniyar cuta kamar gurguwa da ƙeƙasasshiya marar mai da wadda jelarta ta gutsure ko kuma mai yankakken kunne ko ya tsage, haka nan kuma da dabba mai ƙaho ɗaya ko wassdda ƙahonta ya karye, duk waɗannna nau'o'i na dabbobi ba su halatta a yanka su yanka su lokacin layya.

Haka nan dai mawaƙi ya amfani da alƙalaminsa wajen zayyano misalai na abubuwan da kan iya yi wa dabba illa waɗanda za zsu iya saw a ta ta ƙi karɓuwa wajen yin layya.

Domin dai a daɗa fito da manufar waannan saƙon da ke cikin wannan waƙa, mawaƙin ya yi masu karatu ko sauraro bayanin lokuta da kuma adadin yawan kwanin da shari'a ta amintu da su wajenn yankan layya. Ga ma abin da yake cewa a baiti na 29 da 31 da 32 da 33 kamar haka:

29. Loto na yankam layya ran salla ne,
    Goma ga Zulhijji mu bar mantawa.
31. Wato a ban salla ta idi inda,
    Ya yanka tasa mu ko sai mu biyewa.
32. Wanda ya yo yanka gabannin Liman,
    Ba shi ladan layya kar ku musawa.
33. Ranar biyun salla da kashegarinta,
    Dukka ana yin layya babu hanawa.

A baiti na 29 mawaƙin ya yi ƙoƙarin bayyana wa jama'a lokacin da kuma kwanan da shari'a ta tsara domin yin layya. Wannan lokaci da kuma kwana su ne ranar salla babbawadda take farawa tun daga Goma ga Watan Zulhijji.

Amma a baiti na 31 kuwa ya yi wa al'umma bayani ne kan lokacin da dace su fara yanka dabbobinsu na layya, wanna lokaci kuwa shi ne bayan an gama sallar Idi ranar layya.

Daɗin daɗawa a baiti na 32 mawaƙin yana yi wa al'umma dangane da lokacin da ake fara yin yankan layya dole sai an jira Limamin gari ya fito daga masallaci sannan ya fara yanka tasa dabbar, sannan kowa ya yanka tasa, wannan shi ne ya dace da sunnar Ma'aiki (S.A.W.).

A dai ƙoƙarina na isar da saƙon a cikin wannan waƙa ya sake bayyana wa al'umma yadda ya kamata a kasafta laman layyar da mutum ya yanka. Wannan kuwa ya zo ne a baiti na 37 zuwa baiti na 45. A cikin waɗannan baituka ya nusar da jama'a cewa ana raba wannan nama na layya zuwa kasha uku yayin da kashi guda na naman kyauta za a yi da shi, kashi na biyu kuma a yi sadaka sannan kashi na uku mai layyar ya ci kayansa.

Amma idan mun kalli baiti 39 mawaƙain ya yi bayani cewa Kkason da za a yi sadaka da

shi a layyar shi ne wajibi a fidada shi ga ma abin da yake cewa.

39. Abin da ya zama wajibi a cikinsu,
Shi ne Kason sadaka da zaka fitarwa.

Abin da za a nan shi ne idan mutum ya yanka layya zai raba naman nan gida uku daga cikin kaso ukun wadda ya fi kowanne muhimmanci shi ne wanda zai yi sadaka da shi, domin shi ne wajibi miye da sauran kaso biyu.

Bayan mawaƙin ya zayyano mana lokacin da za a yi yankan layya da irin dabbobin da suka wajaba a yanka da kuma yadda za a yi da naman idan an yanka. Daga nan sai kuma ya shiga bayani kan waɗanda shari'a ta yarda a ba wa wannan nama na layya domin a taimaka musu. Wannan kuwa ya bayyana ne a baiti na 40 kamar haka:

40. Lallai ba wa mabuƙaci talaka,
Shi ma fa yawunsa ya zam maidawa.

Haka za lika da cikin dai fito wannan jigo nasa mawaƙin ya ƙara bayani ga wanda ya yanka layya cewa wannan naman layyar zai iya ba da shi ga mutumin da ba addininsu guda ba. Wannan kuwa ya zo ne a baiti na 42, ga ma abin da yake cewa.

42. Kyauta ta naman layya fa in kai niyya,
Har kafiri, ka ba wa babu hanawa.
43. Amma idan kun zam wuri ɗaya zaune,
Ko ya ziyarci gidanka don gaisawa,
44. Ka da ka kai masa har gida a'a,
Wannan abin ƙi kar ka fara yiwowa.

Haka nan mawaƙin ya ci gaba da kawo bayanai da misalai na daban-daban duk dai domin ya bayyana wa mai karatu manufarsa a cikin waƙar. Alal misali akwai wasu wurare da ya yi bayanin kan mutanen da ake yankawa layya, sannan kuma ya yi bayani yanda ake sallamar waɗanda suka yi hidimar aikin naman layyar kamar mahaucin da ya yi aikin layyar, wanda ana iya ba shi kuɗi, amma ba nama ba amma za iya ba shi nama amma a matsayin sadaka ba a matsayin ladan aikin da ya yi ba. Sannan a ƙarshe ya yi bayanin cewa hatta fatar dabbar da aka yanka domin yin layya ba ya hallata a sayar da ita.

Haƙiƙanin gaskiya duk wanda ya karanta wannan waƙa zai fahimci cewa mawaƙin ya yi namijin ƙoƙari wajen fito da abubuwa dalla-dalla a dukkannin baitocon waƙarsa, domin fito mana babbar manufarsa a cikin wannan waƙa.

## 1.8 Kammalawa

Wannan bincike mai taken "Tarken Jigogin Addini Cikin Wasu Waƙoƙin Malam Nasiru Garba Ahmad 'Yan'awaki" ya yi nazari ne kan jigogin addini da suka bayyana a cikin wannan waƙa. An zaɓi waƙai guda ɗaya, wato Waƙar Layya, inda aka gudanar da tarke domin fito da manufar da ke cikinta. Binciken ya gano cewa, wannan waƙa tana ɗauke da babban jigogin addini wato Layya. Saboda haka, za a iya cewa wannan waƙa Malam Nasiru Garba Ahmad ya taka muhimmiyar rawa wajen faɗakarwa da ilmantarwa da al'umma kan muhimmanci yin layya.

Wannan takarda mai taken "Tarken Gigogin Addini Cikin Wasu Waƙoƙin Malam Nasiru Garba Ahmad 'Yan'awaki", an yi ƙoƙarin zaɓo wata waƙa guda ɗaya inda aka yi tarkenta, ta hanyar fito da abubuwan da suka shafi jigon Addini.

**Manazarta**


Abubakar .A T. (2014) Kamusun Harshen Hausa. Zaria: Kamfanin Buga Littattafai Na Nijeriya Ta Arewa.

Abubakar, M. S. da Yahaya, U. F. (2013). Gudunmawar Rubutattun Waƙoƙin Na Siyasa Wajen Samar da Ingantacciyar Dimokaraɗiya. A Cikin Studies in Hausa Language, Literature and Culture: The First National Comference. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Abubakar, N.B. (2013). Gudunmawar Sambo Wali A Kan Rubutattun Waƙaƙin Siyasa : Nazari A Kan Matakan Kirƙiro Jaharmu. A cikin Studies in Hausa Language, Literature and Culture : The First National Conferenc. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Adamu, H. (2011). Waƙoƙi Da Rayuwar Umaru Ɗanbazamfar, Kundin Digiri na Ɗaya. Sokoto: Department of Nigerian Languages. Usmanu Ɗanfodiyo University Sokoto.

Ado, Abdulrahman (2017) Ra'o'in Bincike Kan Al'adun Hausawa. Katsina: Kanki Classical Media Enterprises.

Auta, A. L. (2017). Faɗakarwa A Rubutattun Waƙoƙin Hausa. Kano: Bayero University Press.

Ainu, H. A. (2006). Rubutattun Waƙoƙin Addu'a Na Hausa: Nazarin Jigoginsu da Salonsu. Kundin Digiri na Uku, Sokoto: Department of Nigerian Languages. Usmanu Ɗanfodiyo University Sokoto.

Bashir, I. A. (1999). "Jigon Ilimi Cikin Rubutattun Waƙoƙin Karni na Ashirin: Keɓaɓɓen Nazarin Wasu Waƙoƙin Karni na Ashirin". Kundin Digiri na Biyu, Sokoto: Department of Nigerian Languages. Usmanu Ɗanfodiyo University Sokoto.

Bunguɗu, H. U. (2015). Nazarin Waƙoƙin Bara Na Karni Na Ashirin Da Ɗaya A Zamfara. Kundin Digiri Na Uku, Sokoto: Department of Nigerian Languages. Usmanu Ɗanfodiyo Universty Sokoto.

Bunza, A. M. (1994). Yaƙi Da Rashin Tarbiya, Lalaci, Cin Hanci da Karɓar Rashawa: Cikin Waƙoƙin Sambo Wali Basakkwace. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre Ltd.

CNHN, (2006) Kamusun Hausa Na Jami'ar Bayero, Kano.

Ɗangambo, A. (1980). " Hausa Wa'azi Ɓerse ca. 1800- ca. 1970 : a Critical Study of Form , Content and Style" Kundin Digiri Na Uku, Londn: Jami'ar. SOAS.

Ɗangambo, A. (2007). Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa (Sabon Tsari). Kaduna: Amana Publishers Ltd.

Dunfawa, A. A. (2002). Waƙa A Tunanin Yara. Kundin Digiri na Uku, Sokoto: Department of Nigerian Languages , Usmanu Ɗanfodiyo University, Sokoto.

Dunfawa, A. A. (2013). Balmar Baka:Dabarun Jawo Hankalin Masu Jefa Kuri'a A Cikin "Gaskiya Ba Ta Neman Ado". A Cikin Studies in Hausa Language, Literature and Culture: The Fisrt National Conference. Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.